



# Farin Cikin Da Aka sa A Gabansa

*Yesu ya ɗauki kunyar mu domin mu sami ɗaukakar Sa*



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Ibraniyawa 12:2 ta kira Yesu "shugaban bangaskiyarmu da mai cika ta." Wannan ayar a cikin juyin New International da kuma New American Standard Bible duka sun ambaci Yesu a matsayin "shi ne asali da mai-cika" bangaskiyarmu.

Bari in ƙarfafa ka da waɗannan kalmomin. Duk abin da Yesu ya fara, zai kammala shi. Idan ya fara wani abu a cikinka, zai kammala shi. Wannan shi ne amincinsa—ba wayon mu ba.

Ibraniyawa 12:2 ta ci gaba, da cewa Yesu, "domin farin cikin da aka sa a gabansa ya daure wa gicciye, bai maida shi wani ain kunya ba, a yanzu kuma a zaune yake a hannun dama ga kursiyin Allah." A kan gicciye, Yesu ya daure da kunya, amma bai bari ya hana shi ba. Domin farin cikin da aka sa a gabansa, bai ɗauki kunya a matsayin dalilin da zai sa ya gudu daga manufarsa ba. Menene "farin cikin da aka sa a gabansa"? Farin cikin kawo 'ya'ya da yawa zuwa ga ɗaukaka. Domin ya kawo ni da kai—da miliyoyin wasu irin mu—zuwa ga ɗaukaka, Yesu Kristi ya daure wa kunyar gicciye.

Babu wata mutuwa da ta zama mai ban kunya fiye da ta gicciyewa. Abin kunya ne domin shi ne hukunci mafi ƙasƙanci da aka tanadar wa masu babban laifi. Abin kunya ne saboda yadda mutuwar take kasancewa. Littafi Mai Tsarki ya bayyana a sarari cewa sojojin Romawa sun cire wa Yesu tufafinsa. An rataye Yesu tsirara a kan gicciye a gaban mutane na tsawon sa'oi uku ko fiye. Mutane suna wucewa suna yi masa ba'a. Yaya za ka ji a irin wannan yanayin? A cikin kalma ɗaya: kunya. Yesu ya daure wa kunyar domin ta wurinta ne ya hango cewa, zai kawo mu ga ɗaukaka.

Na gode maka, Yesu, saboda aikinka a kan gicciye. Ina furta cewa Yesu ya jure wa kunya domin ya kawo 'ya'ya da yawa zuwa ga ɗaukaka. Saboda farin cikin da ke gabansa, Yesu ya ɗauki kunyata domin in sami ɗaukakar Sa. Amin.


© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

**Abincin Yini** ★

Kwafi: WD-B097-137-HAU

Sabuntawa ta karshe: 09 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources




© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.